

Musa da Audu abokai ne.



Audu ya zo aji da rake.

Audu ya ba Musa rake.



Musa ya zo aji da lemu.

Musa ya ba Audu lemu.




Musa yana son karatu.

Audu baya son karatu.



Musa ya ci lissafi.

Audu ya faɗi lissafi.



Audu bai ji daƊi ba.

Musa ma bai ji daƊi ba.



Audu yana so ya iya lissafi.

Musa zai taya shi.



Musa na karatu.

Audu na karatu.

Musa da Audu suna karatu tare.